Tayi ihun wahala, amir yayi saurin dawowa wurin ta, yace aunt neena, kinji zafi ne? Neena ta kalle da kyal tace, eh little master, amir ya mika mata hannun sa, yace let me help u, ta rike hannun, zata mike ta sake jin azaba a bayan ta, da sauri ta zauna, har sai da tayi dan guntun hawaye.

Amir na ganin haka, yayi saurin mikewa yayi gun papa dinsa.

Papa stop laughing, aunt neena taji ciwo fa, prince ya kalle ta da gefen ido, yaga yadda take hawaye, yaji dan tausayin ta, dan yasan tiles din dole mutum yaji azaba.

Ya kalli amir, boy wat should I do, ai ita ta jawa kanta ko?amir yayi saurin girgiza kai, noo papa, nina ja mata, aunt neena dont knw hw to run, pls papa help ha, , yayi folding hannunsa, prince ya wani dauke kai, amir ya sake shagwabe fuska, help ha like d way u helped me, lokacin dana fadi a steps.

Prince ya juyo ya kalli ya kalli neena, sannan ya sake kallon amir yace, should I?" Amir yayi saurin kada kai, yes papa.

Prince ya mike yazo kusa da neena, sai daya dan dauki lokaci sannan , ya mika mata hannu, neena tadan kalle shi, kamar kada ta amsa, sai kuma taga bazadai ta iya mikewar ba ita daya.

Ta mika masa hannunta, ba karamin mamaki prince yayi ba, a zaton sa tunda YAR TALAKAWA ce, hannunta will b hard, amma sai yaji laushi, itama neena mamaki taji, danjin hannun prince da tayi laushi kamar ba aikin soja yake ba.

Ya taimaka mata ta mike da kyal, tazo zatayi one step, taji kafarta ta rike, da sauri ta sake komawa ta zauna, ta share hawayenta, sannan tadan jawo kafar ta duba.

Tadan bugu da centre table, amir yazo wurin ta, ya turo bakin sa, kamar yayi kuka shima yace, sorry aunt neena, bari naje na kira grany, a kaiki asibiti, neena ta riko sa, a'a basai naje asibiti ba, idan nasa magani zai daina, ina da magani a daki.

Amir ya sake komawa prince, papa ka goya aunt neena, kamar yadda kamin ranan, she need to go to room, pls papa, prince ya juyo adan fusace, leave me alone kaje ka kira inna ladi ta taimaka mata.

Amir ya zauna, ya hade fuska da gwaiwa ya fara kuka wiwi.

Prince ya girgiza kai, ya mike yazo wurin amir, zan kaita daki, oya bar kukan, amir ya goge hawayen shi yace thank you papa.

Prince ya dawo ya tsaya a kan neena, amir yace, papa muyi sauri, prince ya duka, yasa hannunsa, zai ciccibi neena, tayi saurin matsawa , prince yaja tsaki, ya sunkuto ta, ta ware idon ta̓ , yau itace prince ya dauka???????

Tayi saurin kallon fuskar sa, ya tamke ta tsam, neena ta kura masa ido, wani abu taji ya tsirga mata a zuciyarta,
Tayi saurin dauke kai.

Har daki prince ya kaita, yana kaiwa wurin gadon, ya jefar da ita ya juya ya fice, neena ta murguda baki, kadai kawo ni din, tayi gwalo ˛ .

Sai da tayi ta jinyar jikinta har safe.

Da sassafen prince ya fito da akwatinsa, ya shiga wurin dad yace shi zai koma lagos, dad yace toh shikenan amma biki nan da 2months ya tabbatar ya dawo kafin nan.

Bayan wata biyu°•○●★

Ana ta faman shirye shiryen, daurin auren su faruk da prince.

Iyayen biyu, mum da mami, kullum suna busy.

Zuby da zarah kuwa, lokacin suna semester exams, suma basa da wani time sosai.

Yanzu kuwa neena ta kara wayewa, dan zama da zuby dole mutum ya goge.

Duk kayansu idan sun matse su, ko sun gama yayi, sai ku tarkata su bata, dama neena akwai body, dan jikin ta yafi shekarunta.

Yau ake sa ran zuwan prince, dan sai da dad da abba, suka masa fada sosai, dan cewa yayi, shifa bazai samu zuwa va, suna da aiki a bayalsa.

Amarya ikram, sai shiri akeyi, ta shirya events sunfi biyar.ita kuwa amaryar faruk, Deeja, dama yan maiduguri ne, acan zasuyi komai,sai dai a kawo amarya kawai.

Neena tare da amir a garden, suna wasan buya, yanzu amir a dauke a matsayin uwa, idan bata nan ba mai iya shawo kansa, shi yasa yanzu sai wata wata take samun zuwa wurin umma, kuma ta wayar zuby take samun gaisawa da yaya habu, dan har chat suke da zuby din (toh fa)

Amir yace, aunt neena, yau papa dina zai dawo, neena na shirin bude baki, zarah ta kwala mata kira ta kofar kicin.

Da sauri ta karaso wurinta, zarah dake zuba abinci a plate tace, kije inji mum.

Neena na zuwa, ta samu mun da mami a daki, sun baje kaya a tsakiyar dakin, dama yau

kwanan su biyu da dawowa daga Egypt.

Neena ta gaishe su tace mum gani, mum ta mika mata wasu kayan a dinke suke, kala har biyar, tace ga kayan biki kema, neena tayi murmushi, sannan ta musu godiya.

Tazo zata fita, mum tayi saurin cewa, yauwa neena, neena ta juyo, tace kidan shiga dakin Na'im ki gyara masa, suzy na min aiki a BQ, neena tadan ware ido, dakin papa!!!!! Mum tace eh jeki pls, ya kusan isowa....

By→☆sultana

[8/8, 4:04 PM] .: è è è è
Ĵ *YAR TALAKAWA* Ĵ

By→ _afrah_

Episode →4 + 4 + →4 + 5 +

Neena ta fito, kamar waddda kwai ya fashewa a ciki.

Dakin ta, ta shiga ta ajiye kayan ta, sannan ta fito ta nufi dakin prince.

Tana cikin tafiya suka hadu da zuby, dauke da kedar kayan data amso musu daga wurin tela.

Neena takai hannunta zata taimaka mata, tace barshi neena na kai, kinsan anjima zamu, family dinner, yanzu saloon zamuje, mami tace muje dake, dan haka idan kin gama aikin ki, ki hau taxi kizo, kinsan ai wurin?? Neena tayi murmushi tace ehh na gane wurin, a wuse 2 ko, zuby dake tafiya tace eh nan ne kiyi sauri pls.

Neena ta shiga dakin prince, ta zo wurin gadon sa, ta tsaya, take ta tuna lokacin daya jawo ta jikinsa, ta runtse idon ta, ta bude a hankali, sannan tazo ta fara gyara gadon, kamshin bed sheet din, tamkar shine a wurin , haka nan ta samu kanta da rungume zanin gadon, ta shaki kamshin, ta tuna lokacin daya dauketa, haka jikinsa keta kamshi, tayi saurin ajiye wa, taci gaba da aikin ta, da taga zata fara tunane tunane, sai tace a'uzubillahi minal shaidanil rajim, Allah ka raba ni da tunanin mijin wata, ni duka shekaruna nawa, ni inshaAllah karatuna zanyi nima, na zama kamar mum, tayi murmushin ta taji gaba da aikin gaban ta.

Ta gama kimtsa dakin, ta shiga toilet, woow ta furta, katon toilet ne sosai, gashi shima sai kamshin freshener yake yi.

Ta shiga wanke wa, tana gama wanke na farko ta shiga wurin shower, din, dan daban daban

ne, amma duka a cikin toilet dinne.

Ta shiga ta gama wanke wa, tahau kalle kallen wurin, duk glasses ne, ga kuma remote, neena ta shafa'a da kalle kallen ta.

Sai jin bude kofar toilet din tayi, ware ido tayi, waye ya shigo kuma????

Tayi sauri tadan leko, Prince ta gama a tsale gaban mirror, shaving din kasumbar sa yakeyi, daga shi sai, rigar towel fara.

Da sauri neena ta koma cikin shower din, ta dafe kirjin ta, yanzu ya zanyi, nasan ya prince ya gabe ina nan ciki, zan shiga 6 ne bama 3 ba.

Ta rasa ya zatayi, sai wiki wiki take yi da idanunta.

Shi kuwa prince, yana kammala shaving dinshi, ya wanke fuskar sa, ya juyo yana kallon shower din , da gani nan yake shirin shiga , ya watsa ruwa.

Neena tension dinta ya lunku, dan wanda ke ciki yana iya ganin na waje, shi dake waje bazai ganta ba.

Take wata idea tazo mata, tayi saurin lalubar, aljihun pakistani wandonta, tana tabo wayar dake ciki, ta sauke lumfashin ta.

Wayar amir ce daya bata ajiya, lokacin suna wata a garden, tayi saurin lalubar numbar papa, aikuwa ta gani, Allah ya sota ta iya karatun ta.

Da sauri hannun ta na kyarma ta danna kiran numbar.....

Kuyi hakuri da wannan bana da caji wlh

By→☆sultana

[8/8, 4:12 PM] .: è è è è
Ĵ *YAR TALAKAWA* Ĵ

By→ _afrah_

Episode →4 + 6 + →4 + 7 +

Prince ya mika hannun sa zai bude kofar ya shiga, yaji karar ringing din wayar sa daga daki.

Mtsww, yayi tsaki, zuwa fa wurin nan ba dole bane, ya bude kofar toilet din ya koma daki.

Neeena tayi saurin sauke ajiyar zuciya, wai Allah na gode.

Fitowa tayi da sauri, tazo ta lekasa ta kofar, ganin shi tayi zai dauki wayar, tayi saurin rakubewa, ta fito tana bin bango, tana sando, kamar wata munafuka.

Prince ya dauki wayar, hello dear, am busy nw, zan neme ka anjima kaji, prince bai jira jin komai ba ya kashe wayar, ita kuwa neena hankalinta na, wurin kawai taga ta fice daga dakin.

Sai lallabawa take yi tana bin bango, prince na ajiye wayar ya juyo zai koma toilet, sai ganin neena yayi ta lallabawa zata fice, ya saki baki, ita wannan kuma fa?! Kaman ya make ta yake ji, ya daka mata tsawa, kee!! Mai ya kawo ki nan?!!

Neena ba karamin tsorata tayi ba, ta jingine da hango tana kallon shi a tsoracen.

Prince ya karaso wurin da take a tsaye, ya nuna ta da yatsa saLJ - , mai ya kawo nan?, neena ta kasa motsa harshen ta, dan nauyin da yayi mata, prince ya sake cewa da tsawa, ba da ke nake ba??!! Neena tayi saurin runtse idon ta, dan tsawar da yayi mata kamar zai hadiye ta.

Tayi kokarin motsa lips dinta, tace , ni ni uhm ni dama ni uhm, mum ce , uhm tace wai, nazo na gyara maka dakin, prince ya wani wurga mata harara, ya juya yace, get out!!!! Da sauri neena tayi gaba harda su tuntube.

Sunje salon, an musu gyaran gashi, su zuby sai yaba tsayin gashin neena suke, zarah kuwa na nan zaune sai waya take da mates dinta, wai ance mata zasuyi paper da yamma, shine take ta kira dan taji koda gaske ne.

Sun dawo gida karfe hudu na yamma, neena tayi dakin amir, a kwance ta iske shi tare da faruk, suna game da ipad.

Neena na shigowa tayi sallama, amir yayi saurin saukowa daga saman gadon, ya rungume ta, neena tayi murmushi, my little master, muje nayi maka wanka, amir yayi tsalle zanje naga fuad yau inji uncle faruk, neena tayi murmushi, sanna ta kalli uncle faruk, ina wuni ya faruk? Faruk ya juyo ya kalle ta, yayi murmushi, lafiya neena, har kun dawo ne? Neena tace eh yanzun nan muka dawo, faruk ya mike, bari na shiga wurin ya prince, ya fice.

A zaune ya iske prince, yasha wankan shi, cikin wasu tsadaddun kaya, farare, faruk ya samu wuri ya zauna, yace ya prince , su dad sunce idan mun kammala mu same su a can family house, prince ya tabe baki, faruk yayi dariya ya mike, haba yaya kadan saki fuska, kada ka bawa amaryar mu tsoro, prince yaja tsaki ya jefe shi da remote din da ke kusa dashi, faruk ya fita yana masa dariya.

Neena zaune ta gama shirya amir, yayi kyau shima sosai, ta shafa fuskar sa, little master kayi kyau abunka, amir ya shafa fuskar ta itama yace, u r pretty like a barbie aunt neena, neena tayi dariya, nagode, oya maza je wurin su antu zarah su tafi dakai, amir ya make kafada, ni

sai dake zan je, neena zatai magana, mum ta shigo tare da zarah da zuby.

Mum ta kalli neena , ya baki shirya ba neena, oya tashi tashi, kije ki shirya, dan dole sai ke amir dinnan. Amir ya rike hannun mum yace, grany da aunt neena zamu ko? Mum tace eh da ita zamu, sannan ta kalli neena tashi kije ki shirya.

Neena ta saka, riga da skirt dinta, dinki zamani, sun zauna mata sosai, kamar ba ita ba, sai juyi take tana kallon kanta, wai dama umma na na nan, ta ganni cikin kayan nan, tayi murmushi.

Zuby ce ta shigo dakin, neena kiyi sauri muje, tsayawa tayi tana kallon yarinyar, baki a bude, tace kin ganki neena, neena tayi murmushi tace kinyi kyau kema anty, zuby ta karaso ciki tace, sai dai bakiyi make up ba, kuma dankwalin ki, zuby ta sa hannu ta cire jakwalkwalon daurin da neena tayi, tace zauna na gyara miki.
Neena na murna ta zauna.

By→☆sultana
[8/8, 4:13 PM] .: è è è è è è è è è
*YAR*
Ĵ *TALAKAWA* Ĵ

By→afrah

Episode→4 + 8 + →4 + 9 +

Zuby cikin mintuna kalilan, ta kammalawa neena simple but pretty makeup, woow zuby tace, kin ganki kuwa?, neena sai murmushi takeyi, dan tunda take ,daga powder sai mai , kawai take shafawa fuskarta, yau gashi harda su pink janbaki, tayi kyau mashaAllah, kamar ba ita ba.

Zarah ce ta shigo dakkn, cikin shiri itama, dinkin su kala daya da zuby, tace kuzo muje mana, su mum duk sun wuce fa.

Sakin baki tayi tana kallon neena, ta nuna ta da yatsa, who is dis sisi? , zuby tayi dariya, amir nanny, zarah ta matso tace, dama kyaun neena yakai haka?, neena tayi murmushi tace anty kuma ai kunyi kyau, zarah tace toh matso muyi selfie kafin mu wuce, zuby ta matso hakama

neena, zarah ta daga wayarta ta dauke su, sunyi kyau kamar wasu flowers (lols).

Sun isa wurin mutane a cike, duk family dinsu ne a wurin, amarya ikram tasha gayun ta, cikin wasu tsadaddun kaya, ga makeup an mata, tayi kyau sosai abunta, ango kuma ga kyaun amma ba fara'a, fuskar nan kamar kullum, a tsoke.

Neena ganin duk ba wanda ta sani, kuma duk inda tayi sai an kalle ta, wasu a zaton suma , irin ruwa biyun nan ce, dan a gaskiya neena farace soaai.

Neman su amir ta farayi dan ta tsare su, kada suje su tafka banna, mum ta hango ta, ta kwala mata kira, neena ta karaso wurin table dinsu mum, zaune suke su hudu, mami, mum, mummy, sai wata mata, da ganin kaga su abba, dan kamannin su harya baci, neena ta gaishe su, mum ta mika mata car key, je ki dauko min, wasu kaya a mota, neena ta amsa tace toh.

Wannan matar mai kama dasu abba, tace asiya (mum) ina kika samu yarinya,? Mum tace nanny din amir ce, da sauri naga matar ta kalli mum, nanny? ? Shine taci gayu haka, bata da uniform ne ko me?, mami tace tana dasu, amma su abban faruk sunce kada ta ringa sakawa, matar nan dama da ganin ta yar masifa ce, dan fuskarta ba alamun wasa ko kadan, tace ban gane kada tasa ba, ita din yar Wacece??? Mummy dake jinsu tace yar wacece fa fashe _YAR TALAKAWA_ matar nan ta maimaita, yar talakawa, shine zasuce kada tasa uniform, wannan yar yarinyar da ba'a gama rainon taba shine zaku bata rainon wani?, gata yar talakawa, ko karatun kirki batayi ba, tazo ta koya wa yaro tabi'a irin tasu?, toh wai ina professionals nannies, dinda kuke masa hiring? .

Mum tace yaya B , wannan da kike gani duk tafi su wlh, yaya B taja tsaki, zamuyi dai maganar idan mun isa gidan.

Duk wannan maganar da yaya B keyi, neena taji, dan ta dawo daga daukar kayan taji ta tana aibata ta, a sanyaye ta kawo wa mum kayan, yaya B ta watsa mata kallon tsana, ta juya zata koma seat dinta, batasan lokacin da hawaye suka sauko daga idon taba, can baya ta samu ta zauna, ta buga uban tagumi, hawaye na fita daga idon ta, tunda tazo family duka suna sonta, amma da gani ranar tafiyarta ya kusa, wani kuka yazo mata, tayi saurin dukar da kanta, ita kam bazata iya rayuwa ba amir ba, haka takeji har zuciyarta.

Tana nan zaune gaji anyi kiran amarya da ango, ta dago kanta ta kallo su, sunyi mugun yin kyau , ta dauke kanta tace, ku kam kunji dadin ku.
Tana nan zaune har aka kammala family dinner din nan.

Su zuby suka fara neman ta dansu koma gida, sai suka hade da wasu cousins dinsu, meera da meena, nan suka fada firar yaushe gamo, ya faruk yazo yace musu suzo ya maidasu gida, nan suka bisa, suka ma manta da neena.

Amir kuwa yash neman neena bai ganta ba, su abba zasu koma suka tafi dashi.

Duk wurin an watse, neena ta mike ta shiga neman amir, amma duk wurin sai data duba bata kansa ba.

Tazo har bakin gate tayi tsaye, kowa ya tafi, ita tana can ta lula duniyar tunani, addu'ar ta

daya Allah yasa amir ya bi wasu yana gida.

Can ta matso dan ta tari mai taxi, Allah ya taimake ta tana da sauran canjin dazu, data je saloon.

Wata bakar motace tayi parking a gaban ta, saurayin dake ciki ya fito, tana ganin sa, ta gane shi, Moha ne yayan ikram.

Ya fito ya nufo ta, sai wani layi yakeyi, da gani dai yayi dan shaye shayen sa.

A gaban neena ya tsaya kikam, tadan matsa kadan ta gaishe sa, ya amsa yana dariyar shakiyan ci, yace muje na kai ki gida, neena tace nagode amma kaje, zan hau taxi, moha ya sake matso ta zai kama hannunta, muje bana baby, neena tayi saurin ja baya tace da Allah malam nace kaje bazan bika ba!!

Moha ya kwashe da dariya, see dis village gal, ke harni zance kizo na baki lift kice bakyaso, who d hell r u, yar talakawa dake, bakauyiya.

Neena ta share hawayen ta, tayi gaba dan samun taxi, sai dai jin hannun moha tayi, ta cafko ta, yana neman rungume ta, ta fasa kara ta fara tura shi, dankwalin ta ya fadi, moha ya kurawa fuskar ta ido, ya yaye gyelen jikinta ya jefar , yasa hannunsa yana shafa gashin kanta, neena sai mutsu mustu take tana kuka, can taji kamar yana shirin zage mata zip, tayi kokari ta wanka masa mari, kai wane irin maye ne eyee, moha ya ciji leben sa yace yanzu zaki gane wane irin mayen ne ni, yayo kanta kadan kadan.....

Prince zaune a family house, ajiye coffee cup din hannunsa yayi, ya mike, its over tunda naji shiru.

Ya mike ya dauki, wayar sa ya fito, yasa key ya rufe gidan, sannan ya nufo gate dan a waje yayi parking din motar sa.

Tunda ya nufo gate din yake jin kukan mace, ya kara sauri, yana isa ya hango moha sai kokarin yage wa yarinya riga yakeyi, shi baima gane wacece ba.

Yana isowa moha na yage hannayen rigar neena, dan materials ne, ba wani wahalan yagewa gare shi ba.

Prince yayi saurin zuwa ya janye moha, ya wanka masa kyawawan mari kuda uku, sannan ya tsukomo rigar sa, ya nuna sa da yatsa, kada ka sake na kara maka ma moha, maza wuce jahili kawai, moha yayi saurin shigewa mota ya wuce fuu, dan yasan halin prince sosai, zai iya kai shi sell ne kawai ya rufe.

Juyowa yayi wurin yarinyar, yaga wayam sai gyelenta da Ů da dankwali, can ya hango ta tana tafiya kamar zata fadi.

Neena duk hankalin a tashe yake, gaba daya kwakwalwarta ta tsaya cak, ko prince dinma bata gane shi bane, tafiya kawai takeyi.

Harya shiga mota zai wuce abunsa, can ya fito ya dawo ya dauki, gyelenta da jaka da

dankwali, ya koma motar, yaja yakai dai dai inda take, yayi horn, yaga bata tsaya ba, yajaa tsaki , shi kawai tausayi ta basa, ganin ta yar teenager, ya fito yace kee!!! Neena taci gaba da tafiyar ta kamar zombie.

Prince yasha gaban ta, sai a sannan ta tsaya ta dago idanunta da suka rine zuwa jajaye, fuskar nan kamar tomatoe dan ja.

Prince ya kura mata ido, shikam kamar yasan wannan fuskar, take ya tuna dazun daya ganta a dakinsa, yace a fili nanny! !!! Toh mai ya kawo ta nan ? kuma ya akayi kowa ya tafi sai ita aka bari??

Aka°•○sultana

[8/8, 4:20 PM] .: è è è è è è è è è

*YAR*

Ĵ *TALAKAWA* Ĵ

By→afrah

Episode→5 + 0 + →5 + 5 +

Ya kura mata ido, da gani hankalinta har yanzu a tashe yake, yace da silent voice dinshi, muje ya nuna mata mota, neena tayi saurin ja baya, har tana faduwa, dan gani takeyi kamar har yanzu moha dinne.

Prince ya girgiza kai, yaja tsaki, wai meyasa ma ya tsaya taimakon ta, ya bude kofar motarsa zai fice abunsa, sai kuma ya nushi motar ya dawo wurin ta, har lokacin tana nan a kasa ta zauna rashe rashe , sai kiran sunan Allah take , da yaya habu da umma.

Prince ya duka daidai fuskarta, ya kura mata ido, yace come back to ur sense, nine papa din amir, neena zata ja baya , prince ya rike ta , yace ba abunda zai faru dake, tashi mu tafi gida wurin amir, tayi saurin kallon shi, tace amir, prince ya kada mata kai, ta mike tace ka kaini wurin amir, prince ya mike shima sannan yace shiga muje toh, taki motsawa daga inda take, prince ya buga kafar sa , yace ohh darm it, ke nifa zan wuce abuna haba!

Neena ta kalle shi, prince yace nibar kallona da wani idon ki katoto, neena tayi one step dan zuwa shiga motar, duk ta takure dan sanyin da takeji, ga iska, ga kuma ba gyele a jikin ta bare dankwali, prince ya lira da hakan, sai ya biyo bayan ta dan ya bata gyelen ta rufa, aikuwa neena na juyowa, sukayi karo da prince, dago kanta tayi ta kalle sa, kamshin nan nasa yasa, tayi saurin kallon fuskarsa, tace Papa!!! A zaton ta a zuciya tayi maganar, sai dai taji yace, ke lafiyanki, dare keyi fa, neena tayi saurin shigewa motar, dan take ta dawo hankalinta, prince ya tabe baki ya jefa mata gyelen ta, ta window.

Suna ta tafiya shiru, ita duk ta takure wuri daya, sanyi takeji kamar mai, gashi ya kunna AC abunsa.

Yana lura da yadda take kyarman sanyin, amma saboda mugunta ta prince , sai ya share ta, wai dolene ma ya bata punishment, tasa ya bata time dinsa, gashi yana da abunyi gobe da safe.

Sunzo bakin gate , amma a kulle, dan dare yayi sosai, karfe, sha biyu, yayi kiran wayar mai gadi, shiru sai ringing kawai takeyi, yaja tsaki mtsw...., neena tayi saurin kallo shi, ya sake kiran faruk shima tayi ringing harta katse ba'a dauka ba.

Duk yan gidan sai daya kirasu amma, ba wanda ya dauka, sai tsaki yake take ja, neena data kagara tabar motar, sai tace, papa ni zan shiga ciki, prince ya watso mata harara, sai ki shiga ai, neena tasa hannu ta bude motar, ta fita taje bakin gate din, sai kiran mai gadin take amma shiru, ga iska sai hurata takeyi, sai da tayi minti sha bakwai, sannan ta jingina da gate din, prince ya hurar da iskan bakin shi, yayi mata horn.

Ta kallo shi ,sannan ta karasa wurin motar, shigo kawai prince yace mata, ta bude ta shiga, prince yaja motar suka bar unguwar.

Neena gaban ta yahau faduwa, ina zai kaita ne????

Toh fa nima afrah, na kunna motata nabi bayan prince, dan gano wa idanuna inda prince zai kai mana neena.

Aka°•○sultana

[8/9, 8:19 AM] .: è è è è è è è è è

*YAR*

Ĵ *TALAKAWA* Ĵ

By→afrah

Episode→5 + 6 + →5 + 8 +

Sai sharar gudu yakeyi, ga titin ba kowa , saboda dare ya tsala sosai.

Bai zarce ko ina ba, sai family house din da suka baro.

Ya shiga yayi parking, sannan ya fito ya nufi cikin babban gidan, neena ta bishi da kallo, harya isa babban balcony din gidan ya zura key a kofar yana budewa.

Ganin zai shige, ga tsoro har yanzu bai sake ta ba, yasa tayi saurin fitowa tabi sa ciki.

Babban falone sosai, can ta hango prince yana hawa benen, tayi sallama ta karaso falon, prince bai ko juyo ba ya shige wani daki dake kusa da benen.

Neena ta samu saman carpet ta rakube tadan kwanta, Allah yaso ta ma bata sallah ranar, sanyi takeji bana wasa ba, sai kyarma takeyi, ta rufa da dankwalinta amma inaa, sanyin yaki raguwa, tun tana kalle kallen falon, tana rawar sanyi har barcin dole ya dauke ta.

Prince ya sauko dauke da blanket a hannun sa, daga shi sai singlet, shikam yana son lokacin sanyi sosai.

Yana isowa ya duka wurin da take a kwance, ya warware blanket din, ya rufa mata a jiki, yazo rufawa hannun ta, yaga karcewar akaifa, jini yadan bata mata gyelen data rufa dashi.

Mikewa yayi zai koma sama abunsa, sai kuma ya dawo, yaje ya dauko akwatin gaggawa, ya duka yasa hannu ya janye gyelen, farar soft fatar ta , ta fito, ya dauko auduga da dan spirit, ya fara goge ciwon, neena taji dan zafi, ta muskuta ta juya, juyawan da tayi, ya bayyanar da kyakkyawar fuskarta, da tayi jaa, prince ya kura mata ido, sawon hannu ya gani a jikin fuskarta, ya kai hannunsa ya shafi wurin, ya tausayawa yarinyar gaskiya, gata karama (a yadda kake gani ba).

Ya mike ya wuce saman ya kwanta shima.

Tunda asuba, daya fita sallah, ya barta sai sharar barci takeyi.

Yana gama sallah ya nufi wani dan boutique, kusa da gidan, ya siyo riga da skirt, masu kamar suwaita, amma gaskiya sun hadu karshe.

Yana komawa ya iske ta a zaune a kasan, tayi saurin gaishe shi, ya kalle ta kawai ya mika mata ledar hannunsa, ta amsa, tace miye?, prince yayi gaba bai ko amsa mata ba.

Neena ta bude ledar taga, kayan dake ciki, ba karamin kyau suka mata ba , ta mike ta fara neman inda zata shiga ta canzo kayan, amma duka kofofin a rufe suke, sai dai ta samu bayan kujera , ta fara cire skirt dinta , ta canza, sannan ta zage zip din rigarta , ta cire, ta dauko sabuwar ta saka kanta, harta zura hannayenta....

Prince ne ya sauko cikin dan sauri, ta bayan kujerar ya biyo, baima san akwai mutum a wurin ba...
Neena na ganin yayo wurin ta, ta saki ihuuuu...
Prince yadan tsorata, dan shima bai tsammanin mutum a wurin ba, ta juyo yana kallon ta....
Neena tayi saurin juya masa baya, tana kare kirjinta, prince yaja tsaki, kee kiyi sauri ki same a mota, mu koma gida kafin kowa ya tashi.
Neena tayi saurin kada masa kanta, shi kuma fice, yana cewa idan kin fito ki rufe gidan.

Yana zaune a mota, ta karaso, wani irin kyau tayi a cikin English wears dinnan, prince yadan

kalle ta ya kauda ido, neena ta shiga motar, suka hau hanya.

Suna isa mai gadi ya bude musu, suka shiga, yayi parking ya fito itama ta fito, yayi hanyar baya, itama ta bisa, yazo zai shiga ciki, neena tace, ga keys din, ta mika masa, tsayawa yayi, ya juyo ya mika hannunsa dan ya amsa...

Faruk ne ya fito daga side dinsu, yayi shirin tafiya motsa jiki, ya hango prince da neena a tsaye, wani abune ya tsaya masa a wuya, miye hadin ya prince da neena?, kuma ya akayi suke tare da sassafen nan?

Hannunsu ne ya hadu da juna, wani yarrrr sukaji a tare, kamar shocking, prince ya juya ya shige, itama ta shiga.

Direct dakin amir ta nufa, Allah ya so su ba wanda ya farka a gidan, tayi masa hot milk ta kai ta ajiye masa, sannan ta koma dakin ta, ta cire kayan da prince ya bata, ta shiga tayi wanka ta saka wasu kayan. Wadan da ya bata kuwa sai ta linke su, tace idan mun sake haduwa sai na mayar masa.

Aka°•○sultana

[8/9, 8:19 AM] .: è è è è è è è è è

*YAR*

Ĵ *TALAKAWA* Ĵ

By→afrah

Episode→5 + 9 + →6 + 0 +

Ikram kwance a makeken gadon ta, mummy ce ta shigo dauke da tray , ta zauna a bed side din.
Hannun tasa ta dan bubbuga ikram.
Wake up, tashi kisha maganin nan.
Ikram ta bude idon ta, da kyal, ta mike, tana hamma tare da mika.
Mummy, nifa na gaji da shan wadannan magungunan da kike dirka min.
Mummy tadan buge bakin ikram, banason iya shege, duk ba taimakon ki akeyi ba.
Ikram ta turo baki, ni mummy toh ki daina bani mai dacin nan.
Mummy ta mike tace, gaya nan kisha, saura kuma nazo na iske baki shan ba.
Mummy ta fice.
Ikram ta mike ta sauko daga gadon , tazo ta dauki cup din tadan kurba, tana yamutsa fuska.

Wani daci daci taji yana yi, da sauri ta nufi toilet ta zubar, ta kalli na cup din tace, Allah ya sawake nasha wannan dacin yuks, ta tufar da yawo.

Family gaba daya sun taro a falon dad, breakfast sukeyi, prince na gefe yana shan tea, yaya B ta matsa masa ya zauna, dan shi har ya fito da shirin fita.

Yaya B ta kalli zuby, ina shi amir din yake?
Zuby tace tana cin soyayyen kwai, yana wurin neena.
Yaya B ta daure fuska, wacece neena?
Zuby tace nanny din amir din nan.
mum ta kalli mami, suka hada ido.
Yaya B ta kalli dad da abba, yaza ku kawo yar kauye, yar talakawa ta kula da amir?, yarinyar da ko ita ba'a gama rainon taba!?
Abba yayi murmushi, yaya B ai taimako ne, kuma gaskiya yarinyar na kokari.
Yaya B taja tsaki, duk yawan professionals nannies din da akwai, sai ku rasa wadda zata kula da yaro sai yar karamar yarinyar nan.
Dad ya ajiye cukalin hannunsa.
Ya kalli yaya B yace, mu mun dauki yarinyar nan ne a matsayin yarmu ba'a mai raino ba.
Yaya B tayi saurin kallon dad, yar ku, kun hada dangi ne da ita? Ko kuwa dai kalan dangi?, toh bara kuji, idan har kuna son yarinyar nan taci gaba da kula amir, sai tasaka uniform, kowa ya shigo yasan matsayinta, dan bakuji yadda yan'uwa jiya akai ta maganar ta ba.
Abba zai magana dad ya dakatar dashi.
Dad yace zata saka uniform, shike nan ko? Yaya B ta juyar da kanta tace shikenan, kuma dole asa mata ido dan irin wadan nan yaran ba abun yarda bane.

Prince gaba daya maganar su yayaB kuleshi tayi, ya mike a hanzarce yace, am off, yayi gaba.
YayaB ta tabe baki, shi wannan har yanzu bakar zuciyar na nan?
Duka falon sukayi banza da ita.

Neena ta gama bawa amir abinci, ta zauna taci nata.
Amir ya fita yaje ya gaida kakannin sa, yana dawowa yace wa neena kije YayaB na kiran ki, gaban neena ya fadi? Tasan wannan matar ce, amir ya dafa ta, tana da kirki, zata baki sweet.
Neena tayi murmushin dole kawai ta fice.

A hakimce ta iske yayaB a zaune saman seater.
Dakin ta babban gaske ne, neena ta durkusa ta gaida ita.

YayaB ta amsa a dakile, ta jefa mata leda, wadan nan kayan su zaki ringa sawa yanzu, neena tayi murmushin ta mai sanyi, tace toh.
Sannan ta mike ta fice.
Tana zuwa dakin ta, ta bude kayan, uniform ne, riga ja da black skirt, kala uku ne.
Neena ta cire kayan jikin ta, ta saka uniform din, tazo gaban mirror ta tsaya.
MashaAllah kayan ba karamin amsarta sukayi ba, dan jikin ta, mai kyau ne duk kayan data saka sai sun amshe ta.
Wani murmushi ta saki, tace , ni wadan nan dinma sunfi mani.

Anyi events biyu, amma duka na amarya ne da abokanta, ko su zuby basuje ba.

Yadda neena tayi tsammanin, yayaB zata takura ta, sai taga bata ma damu da ita ba, kullum tana dakin ta tare da amir, neena kuwa kullum cikin mata hidima take, dan ta lura matar nada son girma.

Yau ana gobe daurin auren su prince.

Gidan gaba daya a cike yake.
Neena ta shigo dakin yayaB, ta kawo mata farfesun kayan cikin data sata ta mata.ta ajiye mata a saman table, yayaB dake kallon news tace, zo nan , neena tazo ta zauna a kasan carpet, yayaB tace ina mahaifanki suke? Neena tace da mahaifiyata nake zaune sai yayana, yayaB tace ina mahaifinku? Neena tace muma bamu sani ba.
YayaB ta sauke lumfashi, zaman da tayi da neena ta gane cewa yarinyar mai shiga rai ce, kuma tana mata kamanni da wata data sani.
Ta sauke ajiyar zuciya tace, kina karatu ne? Neena tace na fara amma ban kammala ba, yayaB ta kura mata ido can kuma tace , tashi kije, neena ta mike ta fita

Da daddaren ranar, prince ya shigo dakin yayaB dan amsa kiran ta.

Ya samu wuri ya zauna, yace gani, yayaB ta tabe baki, kai wai wane irin mutum ne eyee? Prince ya kalle ta yace, ni mutum ni irin ki, yayaB tayi dariya, Allah ya sawake na zama irin ka, prince yayi murmushi, yayaB tace duk wannan kumbure kumburen naka bazai hana gobe a daura auren nan ba na'im.
Prince ya daure fuska, wai maina tsare muku ne ?, yayaB tace, ja'iri kana so kana kaiwa kasuwa, yarinya irin wannan., prince ya dakatar da ita, ni zan tafi idan kin gama.
Ya nufi kofar fita, dai dai lokacin neena itama , ta sunno kai zata shigo.
tun ranar nan rabun dasu hadu.
Prince yadan kalle ta ya dauke ido ya fice, neena ta karaso ciki , ta amsa sakon da mum ta aiko ta amsar mata wurin yayaB , tayi saurin kaiwa mum din.
sannan ta koma daki cikin hanzari, ta dauki ledar kayan nan da prince ya bata kwanaki, ta nufi dakin amir, dan taga shigar prince ciki.

Aka°•○sultana
[8/9, 8:21 AM] .: è è è è è è è è è
*YAR*
Ĵ *TALAKAWA* Ĵ

By→Afrah

Episode→6 + 1 + →6 + 5 +

Ta bude kofar ahankali, dan tasan amir baya ciki, yana wurin faruk a waje.

Prince na shiga dakin yayi mika, mutum yana barcin shi, aka wani tashe shi, saboda wannan nonsense maganar, ita yaya B dinnan matsalarta kenan pock nosing , a cikin maganar da bata shafe taba, mtsww yaja taki, let me sleep here nasan ba wanda zai san ina nan balle su dame mutum.

Ya daga hannunsa, ya cire shirt din dake jikin sa, daga shi sai three quarter da singlet fara.

neena ta bude kofar ahankali ta shigo, prince najin bude kofa ya juyo, suka hada ido da neena, neena na ganin shi ba riga tayi saurin juya baya, prince irin mazan nan ne masu 6packs, yayi building din jikin shi sosai.

Neena ta dafe kirjin ta dake bugawa, maiya kawo ta, tayi saurin sa hannun ta jikin kofa zata gudu.

Prince ya daka mata tsawa, kee!! Neena ta tsaya amma bata juyo ba, prince ya mike yazo kusa da ita, bugan zuciyar ta ya karu, prince ya rike kugun shi, yace, kee mai kike zo yi anan?, neena ta fara kyarma dan yadda yayi maganar ba wasa, uhm uhm dama kayan nan ne zan mayar maka.

Prince yace wane kaya, neena ta mika masa ledar, prince yaja tsaki, ta haka ake mikawa mutum abu a kauyen ku? Neena ta girgiza kai, sannan ta rufe idon ta , ta juyo ta mika masa.

Prince ya tabe baki, sannan ya amsa ledar ya bude.

Kayan daya bata ne a family house, ya mika mata ledar, mai zanyi dasu, ko kin taba ganina nasa kayan matane? Neena ta girgiza kai, yadda ta rufe idon ta, gashin idon ta masu tsawo suka karawa fuskar ta kyau, prince yadan kura mata ido, ganin girar idon ta, yayi wadda ta fado a kumatun ta, yadan kara one step zuwa gab da ita.

Neena ta sake matse idon ta, tana cewa , wayyo kayi hakuri, ban taba ganiba, a zaton ta bugun ta zaiyi.

Ya mika hannun sa, zuwa fuskar ta, zai cire gashin, zuby ta banko kofar dakin ta shigo, tana cewa neena neena, kizo ga ya abubakar dinku ya kira.....

Neena dake kusa da kofar ta tafi zata fadi, dan bude kofar da zuby tayi, ya turo ta ita kuma.

Da sauri ta ware idonta dan naiman ma kanta madafa, sai kawai taji ta a jikin mutum.

Ta shaki kamshin sa, zuby ta ware ido tana kallon su, wani mamaki da tsoro ya lullube ta, miye haka yake faruwa?

Prince ya ture neena gefe, da kyal ya iya ma turen tan, da duka gabobin sa sunyi sanyi.

Neena tayi saurin juyawa ta kalli zuby, na'am anty zuby.

Zuby ta kalli prince, ya wani watso mata harara, yayi kan gadon ya kwanta, yace ku fice min pls!!!

Sukayi waje da sauri, har suna buge juna.

Zuby kasa tambayar neena tayi, sai dai tayi alkawarin yin investigation akan abunda idon ta ya gane mata.

Washe gari juma'a, 21 of November, misalin karfe biyu da rabi na rana, dubun nan jama'a suka halarci _DAURIN AUREN_ na'im prince da Ikram isma'il.sai faruk da Deeja Aliyu.

Bikin ya tara manyan manyan yan siyasa, da masu hannu da shuni, sojoji dayawa sunzo dan a reception din har pareti akayi.

Da karfe 6 na yamma aka kawo amaryar ya faruk, deeja, ta sauka a gidan abba.
Karfe 8 aka shigo da amaryar prince wato ikram.

Gidajen biyu sun cika sun batse, angwaye kuwa na family house da abokansu, sai washe gari zasu dawo gida ayi budar kai, sannan kowa ya dauki matarsa yakai, gidajen dasu dad da abba suka gina musu.

Umman neena tazo itama, amma basu hade da yayaB ba, dan ita tana family house wai dole ne yaran zamani asa musu ido, dan kada muyi barna.

Neena na kicin tana taimakawa inna ladi suna wanke wanke, bayan ta raka umman ta , tahau mota.

Zarah ta shigo kicin din, tace neena ga waya yayaB zatayi magana dake.

Neena ta goge hannayen ta, ta amsa wayar.

YayaB tace, niimatu kina ji ko, neena tace eh, ki hado min koko da tuwo , zan aiko a dauko minke, ina zan iya da abincin turawan nan duk maso sa basar ne, neena tayi dariya tace toh shikenan nan da awa daya zan kammala, yayaB tace toh kiyi dai sauri yunwa kamar ta zautar dani wlh.

Neena ta nemi taimakon inna ladi, da wata mata da tazo daga garin su dad, suna kwatanta mata har ta kammala duka ta saka a flask ta ruba a kwando.

YayaB na ajiye wayar, ta sauki dan samun wanda zata aika.

Samari ne su hudu a falon, tana saukowa suka gaishe ta, ta amsa, sannan tace musu, akwai wanda yasan gidan bikin cikin ku?, suka kalli juna , suka ce mama bamu kai ga zuwa can bama, yayaB tace hakane kusa baki ne, ina faruk ? Din ne? Sukace yaje siyo credit a waje, yayaB tayi dan tsaki ai shi dama yawo kamar yaci kafar kare.

Ta koma daki dan jiran faruk, amma inaa yunwa ta addabe ta.

Ta fito ta nufi dakin da prince yake.
A kwance ta iske shi, yana kallon sama, gaba daya baya cikin farin ciki, har kamar shi, za'a aura wa wannan yarinyar da ko kamun kai bata dashi.
Jin hannun yayaB yayi, ta riko kunnen shi, yayi yar kara yace, yayaB mai nayi maki, zaki cire min kunne .
YayaB ta zauna tace, tashi na aike ka gida, prince ya zauna yana cewa, ni na gaji ki aiki faruk mana, yayaB tace ni kai nake so kaje min aiken ai.
Sai da tayi ta rokon sa sannan ya yarda zaije.

Neena na nan a tsaye wajen gate, sai dube dube takeyi, amma shiru ba wanda taga yazo.

Can ta hango wata black benz ta nufu ta.
Akayi parking a gaban ta, ta karasa wurin driver din, prince ya sauke mirror, neena tana ganin shi taji gaban ta yadan buga, wani irin kyau yayi mata , tace kodan yau auren shi, shiyasa yayi kyau abunsa.

Ta mika masa basket , ga abincin , prince ya dauke kai yace, waye dan aiken ki???

Aka°•○sultana
[8/9, 8:30 AM] .: è è è è è è è è è
*YAR*
Ĵ *TALAKAWA* Ĵ

By→afrah

Episode→6 + 6 + →7 + 0 +

neena ta kalle shi, hankalinsa na wurin wayarsa, tace ban sanar wa mum ba, kuma zan kula da amir.

Prince ya juyo, ya wani watso mata idanunsa yace, nace kizo muje ne? Neena ta sadda kanta kasa, ita wallahi sometimes, prince dinnan na kule ta, kullum sai iya gwale mutum.

Prince ya tada motarsa, neena tayi saurin cewa, ga abincin nan fa bansa a motan ba, yayi banza da ita.

Taga alamun dai wucewarsa zaiyi, ta bude motar da sauri ta shiga tare da kwandon , sai sauke ajiyar zuciya takeyi, inaa zata kuskure ya tafi, ta bani da masifar yayaB.

Tunda suka hau hanya, bai ko kalle inda take ba, sai tafiya sukeyi kamar kurame, har suka iso, yana parking motar ya fice abunsa.

Neena ta fito, ta dauki kwandon, tabi bayan sa.

A falon suka iske faruk da frnds dinsa, suna shiga yayi sama abunsa.
Neena tayi tsaye dan bata san ina yayaB take ba.
Ta gaishe da faruk da sauran dake wajen, sai kallon ta sukeyi.
Faruk ya taso yazo wurin ta, yace wurin yayaB kika zone? Neena tace eh abinci na kawo mata.
Faruk yayi murmushi ya nuna mata dakin.
Tana shiga yayaB ta mike, yauwa , ta tari neena ta ajiye kwandon a table, neena ta zuba mata sannan ta samu wuri ta zauna.
YayaB na kwasar girki tace, kince ummanki zata zo? Neena tayi murmushi, eh tama zo dazun harta tafi.
YayaB ta kallo neena, shine baki fada min ba?, neena tace ai bakya gidan lokacin, amma tace a gaida ke, yayaB tace ina amsawa naso ai mu gaisa, dan na mata maganar rikon ki, kinsan zaman kadaici na ishe ni.
Neena ta kalle ta da sauri, tace riko? YayaB ta ajiye cukalin hannun ta, tace, ko bazaki bini ba? Neena ta girgiza kai dan mamaki take ji.
YayaB tace, dana daya a duniya, kuma yanzu bama tare da juna, akwai wadda nake nema, nasan idan har na ganta takaicina zai ragu.
Neena ta jinjina kai tace, ina danki ya tafi? YayaB tace yana kasashen nasara, neena ta gyara zaman ta, azuciyarta taji tausayin yayaB, (yayaB ta manyanta sosai, amma jikin ta na nan gwanin sha'awa , yayaB kanwar mahaifiyar su dad da abba ce, itace auta a wurin maman su dad wato kakar su prince kenan wadda ta zasu lokacin haihuwar faruk).
Neena ta mike tace, zan koma, nasan amir nacan na nemana, yayaB ta kurbi ruwa, toh shikenan , na'im zaya maidake, bari na kira shi, neena kamar ta fasa ihu, ita dama ko ya faruk ne.

Ya fito daga wanka kenan, yaga kiran yayaB, yaja tsaki, wannan tsohuwar yar rigima ce wallahi.
Ya dauki wayar yace, kuma ya akayi ? YayaB tace kazo ka mayar da niimatu gida, ta kashe wayar.

Sai daya bata kusan awa da rabi, har neena ta fara gyangyadi ita da yayaB, sanna ya shigo.
Sukayi saurin farkawa, yace muje kawai ya fita, neena tayiwa yayaB sai da safe ta fito.

Sun hau hanya, aka fara zuka ruwan sama.

Har suka isa ana kwara ruwa, neena ta bude kofa tana tsoron kada ruwan ya tabata, prince yadan kalle ta, ya juyar dakai abunsa.

Da kyal ta fito daga motar, dai dai lokacin wata kawar ikram ta fito da umbrella, da gani tafiya zatayi.

Prince sai kallon neena yake yaga ya zatayi da ruwan nan mai karfi, sai yaga tayi tsaye a bakin gate din .

Yaja tsaki wannan ita shes very slow at everything, ya juya seat din baya, ya dauko umbrella ya fito.

Yazo har wurin ta, neena sai binshi takeyi da kallon mamaki, ya mika mata umbrella din.
Kawar ikram ta kalle su, baki bude, ta shige motar ta.
Tana shiga ta kira ikram, ta kwashe gaskiya da karya ta fada mata.

Ikram ba karamin tashi hankalinta yayi ba, lallai kuwa sai ta gyarawa yarinyar nan zama....

Aka°•○sultana
[8/9, 8:30 AM] .: è è è è è è è è è
*YAR*
Ĵ *TALAKAWA* Ĵ

By→afrah

Episode→7 + 1 + →7 + 5 +

Washe gari akayi budar kai, amaren biyu duka sunsha gayu abunsu.
Neena kuwa ko fitowa bata samu yi ba.
General dinsu prince sai ranar ya samu zuwa.
A babban hotel aka saukar dashi, yazo har gida ya gaida su dad da abba, yana yaba irin gwazon prince a fanni aikin su.
Prince gaba daya ranar busy yake, sai da yamma sosai , ya shigo gidan, ya samu mum a daki ita da mami.
Sai daya gaishe su sannan ya samu wuri ya zauna.
Mum tace anya kuwa kaci abinci ma yau kuwa? Prince ya girgiza kai, yace ban samu lokaci ba wallahi, sai dana kai general waheed har airport sannan na samu dawowa gida.

Mum da mami sukace ai gaskiya mutumin nada kirki sosai, kalla fa kayan da ya kawo mana.

Prince yace haka yake, yana kyautatawa soldiers dinshi sosai.
Mum tace Allah ya kara masa budi, mami ta amsa da amin.
Prince ya mike yana cewa, ni na gaji ne over, let me go n hv a rest.
Mum tace sannanu, sai kaje kaci abinci ka huta dan kuna da tafiyar safe gobe.
Su ikram dinma na side din mamin ku.

Prince ya wani dauke kai abunsa.

Mum ta mika hannu ta dauki wayarta, bari na kira zuby ta fada wa neena ta kawo maka abinci.
Prince ya juya ya fita, kamar ya shake mum yakeji.

Yana shiga daki, ya shiga ya watsa ruwa, ya fito ya saka kana nan kaya, ya zauna bakin gadon yana amsa waya.

Neena tayi sallama ta shigo, amir na biye da ita dauke da cup.

Suna ajiye masa, sukayi kofa dan fita, prince ya ajiye wayar hannunsa, yace zoki zuba min.
Neena taji kamar ta ruga da gudu, dan tasan shi ba'a iya masa.

Ta dawo tazo, ta fara zuba masa, amir na gefen ta, yana wasa da dutsunan rigarta.
Tana zubawa tace wannan yayi?, prince yayi kamar baiji taba.
Neena ta kada kai, tace a zuciyarta, ai maza nata ci soaai, ya faruk ma idan yace na zuba masa, dayawa nake zubawa kuma ya cinye.
Ta dauki serving spoon, ta kara abinci, har sai daya yayi suro.
Tace na zuba, ta rike hannun amir zasu wuce.

Prince ya daka mata tsawa, ke dawo !
Neena ta dawo ta tsaya, prince ya nuna abincin yace, ni dawa zanci wannan?, neena tayi shiru, prince yace, kewai komai baki iya bane? Tayi shiru.
Ya kara kulewa, yace, toh sai ki zauna, idan naci wanda ya isheni, sai ki cinye sauran.
Neena ta ware ido, ni naci abinci dazu, prince ya jawo table ya faraci, amir yazo wurin sa yace, papa, anty neena taci nata ita, prince yace, sai ta kara wannan ai, amir yace papa, ya mata yawa, ita ba acici bane, prince yace sai ka taya ta kuci.

Suna nan tsaye, yadan tsakuri abincin, ya tura masa sauran, mai uban yawa.
Neena ta dauka, tace amir muje, prince ya rike hannun amir yace, ba inda zaku, a nan zaki zauna ki cinye shi.
Neena ta bata rai, ita da yanzun nan ta gama shan fura wurin yaya B ga cake din da su zarah suka bata, ko ita rumbu ce ai sai haka, toh ga kuma wannan uwar fried rice din.
Kamar zatayi kuka, ta samu wuri ta zauna, daga waje, mami tayi kiran Amir.
Yayi waje da gudu yana amsawa.

Prince ya haye gadon sa, wayarsa tayi ring.
Ya dauka bakuwar numba ce.
Hello,
Ikram daga dayan side din ta kashe murya, tace hello dear,
Prince yadan daure fuska, pls waye?
Ikram taji wani daci a ranta, mijin ta amma ko numbar ta baya da.
Ta dai yi murmushi tace, ikram ce.
Prince ya tabe baki, ohh toh ya kike.
Ikram ta amsa da lafiya, amma ina son ganin ka pls.
Prince yace a gajiye, ganina ? Me zan miki?
Ikram ta hade miyau da kyal, lallai ma, idan tana son ganinsa sai da dalili tab.
Ta kara tsuke murya, yau frnds dina zasu tafi, suna so kuyi bankwana.
Prince yace am really tired nw, bt zan duba dai.ya kashe wayar.

Neena dake zaune a kasan carpet, tana tsakurar abinci, taji yana ta waya , kuma taji yace ikram, bt bataji ya sukayi ba, dan shi maganar sa silent, ko wace albarka.
Hakanan taji wani abu a zuciyarta, ita dai idan tana tare da shi, she fills save.
Kodan ya taba taimakon tane oho.

Prince yace, kee! Ba tunani na ajiye ki, kimin ba.
 Neena ta samu kanta da shagwabe fuska, tamkar yadda takewa, yaya habu, idan ya matsa mata taci abinci.

Ni na koshi, Allah cikina zai iya fashewa idan na cinye wannan.
Prince ya kura mata ido, hakanan yaji dama, ta

Ta saki wani kukan, ita kam tasan ya prince , ba sonta yake ba, amma yanzu, itama kam ta fara kamuwa sa son sa, dan yadda yake taimakon ta.....

Aka°•○sultana

[8/9, 8:30 AM] .: è è è è è è è è è

*YAR*

Ĵ *TALAKAWA* Ĵ

By→afrah

Episode→7 + 6 + →8 + 0 +

Hannu taji a kafadarta an dafa ta, a tsorace ta juyo dan ganin waye.

Prince ta gani a bayanta, ta ware ido, tana goge su , wai ko gizo ne yake mata.

Prince ya zauna a kusa da ita, (ya kasa barci shine ya fito shan iska, Allah yasa ya hango fitowar ta sashen mami tana kuka).

Yana zama neena ta mike da sauri, zata fice.

Prince ya riko hannunta, ta tsaya cak ta kasa juyowa, prince ya mike ya kusanto ta sosai.

Neena gabadaya taji lumfashin ta na neman ya tsaya, toh mai hakan yake nufi?

Bata idasa tunanin da take yi ba, taji prince ya juyo da ita, ta fada a faffadan, kirjin sa, ta ware ido a tsorace...

Saukar ajiyar zuciyar shi , gabadaya gabobin ta, suka kasa yunkurin kwace kanta daga kirjin sa, ta shaki kamshin sa, ta lumshe idon ta, take taji kamar an dasa mata wani masifaffen sonsa.

YayaB ce tazo wurin window din dakin ta, neena ta manta bata kullo min windows dinnan ba yau.....

Hango su prince tayi, da yake akwai , wutar lantarki ta wajajen, ta haska su.

Ta kura musu ido tana kallo, taji mamaki kwarai, ashe akwai ranar da prince su wata banda nateefa, ta kullo windon ta dawo ta zauna bakin gadon ta tana tunanin wannan al'amari.

Sai da sukayi minti sha biyar a haka,sannan prince yasa hannu yadan matsar da ita, yayi tafiyarsa zai shige cikin gidan, neena tabi bayan sa da kallo, har yakai kofar shiga ya tsaya, ya juyo, shi take kallo, ya sakar mata murmushin da tunda take dashi bata taba ganin yayi saba.

Neena mutuwar tsaye tayi , bata san lokacin da kumatun ta da lips din ta, suka bayyanar da murmushi ba, prince ya juya ya shige ciki.

Yana zuwa dakinsa, ya dafe kirjinsa, sai bugawa yakeyi da sauri da sauri, ya runtse idanunsa, koda yayi soyayya da lateefa, bai taba jin wannan yanayin ba, ya dafe kansa, noo prince u cant fall inlove wit dat small gal, gata _YAR TALAKAWA_ yarinyar da bata waye ba, yarinyar dake matsayin mai rainon danka, yaja tsaki da yaji zuciyarsa ta fara zafi, ya mike ya dauko drugs dinsa ya sha, sannan ya kwanta, wani barci mai dadi ya dauke shi mai tattare da mafalkai masu annashuwa.

Neena ma daki ta koma bayan ta duba amir yayi barci, ta haye saman gadon ta, tana murmushi kamar bakin ta zai yage, ta mike ta zauna tsakiyar gadon, ta dafa kirjin ta, ta runste ido, ta shiga tunano duk wani moments da sukayi da prince.

Can kuma tadan tsaya da murmushinta, mai yasa toh ya rungume ta, kodai tausayin ta kawai yaji, ba sonta yake ba, ta buga uban tagumi tace....

Ya za'ayi kuwa ya prince yaso ta, _YAR TALAKAWA_ da ita, wadda a karatu ma ajin ta uku ta tsaya, ta sauke ajiyar zuciya, shi dake da mata kamar ikram ai bazai taba son mace irin taba (ni kuwa afrah nace, kedai duba mirror _NEENA_)

Tadan buga goshin ta da tafin hannun ta, neena ki dawo daga duniyar tunanin ki.

ikram kuwa neena na wucewa , ta kira mummy dinta, ta fada mata komai tace, mummy ba inda zani da wannan karuwar yarinyar, gara ma kusan abunyi kafin gobe eheen.

Mummy tace, haba ai koni bazan yarda ki tafi da itan ba, zan kira mum dinshi, zamuyi maganar, ba inda yarinyar nan zata biku.

Ikram tace, ni mummy har amir din ma, bana so ya bimu, da rainon shi zanji ko da cin amarcina (kuji fa mutum yana magana da uwarsa amma kamar yana yi da kawar sa zamani kam ya canza).

Mummy tace, hakane gaskiya bari na kira mum dinshi muyi maganar, ikram tace toh mummy , sukayi sallama.

Moha dake zaune kusa da mummy yace, mummy mai ya faru ne da ita ikram dinnan, uwar shaida.

Mummy ta fada masa, ikram na zargin prince da mai rainon amir.

Moha yaja tsaki, dama ashe akwai abunda ke tsakanin su, shiyasa ranar ya bata min show, mummy tace kasan suna tare kenan, moha yace eh mana mummy ranar family dinner, ya ganni tare da ita, shine yazo ya wani kora ni, ashe dama shike nemanta, mummy taja tsaki , kai kuwa mai zakayi da wannan aljanar yarinyar, ga yan'matan a gari, moha yayi murmushi, mummy Allah yarinyar ce akwai kyau, mummy tace ,kadai bi ahankali idan abban ku ya san da wannan banzan halin naka , bazakaji da dadi ba (pls iyaye mata a kiyaye).

Mummy ta kira mum, suka maganar , mum bataji dadi ba ko kadan, tayiwa prince aure ne, dan amir ya samu wadda zai kira uwarsa, amma ba damuwa nan gaba sai yaje, dan maganar mummy tayi tasiri a zuciyar mum, da tace idan amir da neena sukaje, su ikram "bazasu sake da junan suba"

Washe gari da sassafe, aka taru family, a babban falon dad.

Abba yace wa mum, ita neenan ta shirya daiko? Ikram tayi saurin kallon mum, suka hada ido, mum tace ai bada su zasu tafi yanzu ba.

Dad yace kamar yaya? Mum tace wai da idan sunyi dan watan ni sai akai su amir din , abba yace hakan yayi, ikram tayi murmushi ta kallo prince...

Aka°•○sultana

[8/9, 8:30 AM] .: è è è è è è è è è

*YAR*

Ĵ *TALAKAWA* Ĵ

By→afrah

Episode→8 + 1 + →8 + 5 +

Prince ya dauke kai, yayaB ta gyara murya, toh idan dai bazata bi su na'im ba, nizan tafi da ita.

Duka falon aka kallo ta, tace ku kalle ni dakyau, ta kalli abba , yau zamuje ka kaini gidan su, nayi magana da umman ta, ta bani rikon ta, nasakata makaranta tayi karatu itama.

Dad yace , yayaB ai ko anan dinma zamu saka ta, amma raba neena da amir zaiyi wahala.

Abba yace kwarai kuwa, kada ki damu indai karatu ne zamu saka ta tayi inshaAllah.

YayaB tace toh shikenan, dan dai bana son amir yayi rashinta ne kawai zan barta anan.

Abba ya kalli faruk dake zaune suna magana kasa kasa da zarah, yace kai faruk, makarantar nan dakayi service, kaje ka nemawa neena, dad yace kaje ka tambaye ta inda ta tsaya.

Faruk yace toh dad, yaci gaba da maganar su da zarah, yayaB ta kai masa duka, kaji ja'irin yaron nan, an maka magana amma ko tashi bakayi ba, faruk yace, haba yayaB zan tashi mana, yayaB tace ai fah, an zama ango har an fara rashin kunya, nan da jiyane ana fada zaka mike, saura ka zama mijin hajiya...

Aka kwashe da dariya, amma banda prince, mikewa yayi ma zai fita, yayaB tace su oh oh kuma, sai bakin rai, ana so ana kaiwa kasuwa...

Ikram tayi wani fari da ido, prince yace ehh din ina ruwanki, yayi ficewarsa.
Mum tace, ikram muje ki dauko jakar ki , flight din 8 zaku bi, mami ta mike tana cewa, bara na daukowa na'im danbum naman sa.

Prince ya fito da jakar shi, ya bawa faruk yakai masa mota, dakin amir ya nufa dan yi masa sallama.

A zaune ya iske su, suna wasan *X* and *O* a ipad din zuby.
Sai dariyarsu sukeyi, ya tsaya yana kallon su, amir yace anty neena banda cheating fah, neena tace little master, kaima fa dazun kayi , amir ya amshe ipad din ya haye gado yana cewa, toh dukkan mu winners ne, neena ta fara binsa yana guduwa, tace ban yarda ba, dawo mu sake wani...
Suna cikin wasan su, basu ma lura da prince dake tsaye bakin kofar ba...
Sai da zarah tazo wurin tana cewa, ya prince ka fito inji su mum...sai sannan neena ta juyo ta ganshi a tsaye, tayi saurin tsayawa daga wasan da suke, amir yayi wurin papa dinsa, prince ya shafa kansa, ya riko hannun sa, suka fita.
Neena tabi bayan su itama.

A waje faruk ne zai kaisu, mum, mami , zarah, zuby duka ana wajen, yayaB taki fitowa , wai barcin ta zata koma.
Mum ta rike ikram, tace ki kula da kanki dear, ikram tace toh mum, zuby da zarah sukayi hugging dinta, sukace ki kula mana da yayan m